Level 3

Yaya Jiragen Sama ke tashi?

Mawallafi: Aditi Sarawagi
Mai zane: Lavanya Karthik



Sarla tana son kallon tsuntsaye suna tashi.

Wata rana, yayin ajin kimiyya, ta leka ta taga, sai ta ga maiki na yawo a sararin samaniya. Yaya farin cikin tsuntsun zai kasance! Kuma tana son ganin jiragen sama na tashi.
"A nan, menene sunanki? Shin bai kamata ku kalli allo ba? ”
Sabuwar malamar da ke ajin su Sarla ta tambaya.

Sarla ta tashi da sauri ta ce, "Yi hakuri Madam, ina kallon maiki ne. Ina ma a ce muna iya tashi kamar tsuntsu, ko kamar jirgin sama .... "
"Menene sunanki?"
"Sarla."



“Oh suna mai dadi! Shin kin san cewa Sarla sunan mace ta farko da ta fara tukin jirgin sama a kasar Hindu? Sunana, Hamsa, yana nufin agwagwar ruwa. Swans ɗaya daga cikin manyan tsuntsayen da ke tashi ne, kin sani, ”in ji malamin. " Dole ne ki ɗan jima a cikin ɗakin karatu, Sarla. Na tabbata akwai litattafai da yawa game da tsuntsaye da jiragen sama, da kuma na'urorin da ke tashi kamar jiragen sama. ”
Bayan 'yan kwanaki masu zuwa, Sarla cikin farin ciki ta samu ilimi mai yawa game da tsuntsaye, da kuma jiragen sama.

Sarla ta koyi cewa mutane na iya tashi suma, amma ba kamar tsuntsaye ba. Zamu iya tashi zuwa kowane birni na duniya cikin jirgin sama, ɗaya daga cikin manyan abubuwan da ɗan adam yayi.

Tare da taimakon wannan babban inji, zamu iya samun farin ciki na yawo cikin iska. Tsuntsaye halittu ne na sama waɗanda basa buƙatar na'urar waje don tashi. Yawancin lokaci, fuka-fukan tsuntsu sun fi girma fiye da sauran jikinsa. Fuka-fukan suna da matukar rashin nauyi, wanda hakan ke ba tsuntsaye damar tashi.

Jiragen sama suna da girma da nauyi. Kamar dai tsuntsaye, jiragen sama suna da fuka-fukai a bangarorinsa na dama da hagu wanda ke taimaka musu su tashi. Fuka-fukan fikafikan jirgin suna kama ne kamar na tsuntsaye - masu gogewa a saman da lebur a ƙasan wanda ke taimaka ma su wurin tashi sama a sararin sama.

Tsuntsaye suna fyada fuka-fukansu don su tashi, amma ba shakka bamu taɓa ganin jirgin sama yana buɗe fuka-fukansa ba! Tsuntsaye suna fyada fuka-fukansu yayin da suke amfani da iska don tura jikin su sama.

Suma Jiragen sama suna tashi tare da taimakon ƙarfin iska. Wannan na'urar tana amfani da injin da ke cikin jikinta don ƙirƙirar iska wanda ke gudana a ƙarƙashin jirgin sama.



Na'ura wani injin ne mai matukar ƙarfi wanda yake yin aiki kamar kwakwalwar jirgin sama. Kamar dai yadda tsuntsu yake amfani da hankalinsa da dabaru don sarrafa tashinsa, injinona suna taimaka wa jiragen sama su tura su sama da kuma taimakawa su ci gaba da tafiya. Lokacin da injunan jirgin sama suka ƙona mai, suna sakin gas mai zafi a cikin sauri wanda ke tura iska a bayan injinin, yana tura jirgin saman zuwa gaba.

Motoci da sauran abubuwan hawa masu injuna su ma suna tafiya gaba. Amma ba za su iya tashi sama ba kamar jirgin sama. Iskan yana guduna a sama da ƙarƙashin fuka-fukansu wadanda ke kama da fuka-fukan tsuntsu kuma ya ɗaga jirgin sama cikin sararin samaniya kuma ya rike shi can.

Jiragen sama su ma suna da wutsiyoyi, kamar tsuntsaye, don sa su tsaya tsaf kuma su taimaka ma su wurin yin kwana.

#

Jiragen sama suna buƙatar manyan hanyoyi masu tsayi don tashi da sauka. Wadannan dogayen hanyoyi ana kiransu hanyoyin gudu kuma jiragen sama na bukatar tafiya a guje a kan hanyar gudu kafin su iya tashi zuwa cikin iska. Jiragen sama suna buƙatar samun gudu da yawa don ɗagawa sama a cikin iska.

Yawancin jiragen sama suna iya tashi kawai idan suna tafiya a guje. Hanyar gudu muhimmin yanki ne na filin jirgin sama saboda tana ba jiragen sama isasshen lokaci don ƙara saurin suda kuma cirawa zuwa sama.

Jiragen sama sun san inda ya kamata su je saboda matukan jirgi ne suke bi da su. Matukan jirgi suna sarrafa jirgin daga wani wuri a gaban jirgin sama da ake kira cockpit. Suna ci gaba da tuntubar tashar jirgin sama (wani wuri daga inda jirgin sama yake tashi da sauka) ta hanyar ingantattun na'urori na zamani. Kamar dai yadda akwai alamu da 'yan

sanda da za su taimaka mana a kan hanyoyi, akwai masu kula da zirga-zirgar jiragen sama da ke fada wa matukan jirgin lokaci da kuma inda za su tashi; kuma lokacin da babu matsalar tashi ko sauka.

Jirgin sama haƙiƙa babban tsuntsu ne. Ba wai kawai yana da fasali kamar tsuntsu ba, yana kuma bamu damar tashi, duk da cewa ba kamar tsuntsaye ba! Sarla tana son zama matukiyar jirgi kuma ta tuka jirgi idan ta girma.



Shin Ko Ka San?
Jirgin sama na farko a Indiya shi ne Harlow wanda ya fara tashi a cikin watan Yulin 1941.

An fara ba da lasisin tukin jirgin sama na farko a kasar Hindu ga JRD Tata a cikin watan Fabrairun 1929 daga Aero Club na Indiya da Burma.



Jirgin sama mafi sauri a cikin duniya shine Lockheed SR-71 Blackbird wanda ke tafiya da saurin da ya fi na sauti.

Sarla Thakral ita ce mace 'yar kasar Hindu ta farko da ta fara tuka jirgin sama. Ita ce kuma mace ta farko da ta fara samun sama da awanni 1000 na tashi.



Bari mu tashi!

Yi nishadi tare da abokai tare da waɗannan ayyukan:

1. Ku yi jirgin saman takarda don muga wanda jirginsa zai fi tashi. Shin takarda ce ko yadda aka yi shi ne yake sa jirgin

saman takarda yayi sauri? Lura da abin da ya faru lokacin da aka ƙaddamar da kowane jirgin sama. Shin akwai bambanci idan kun busa sama, ko ciki ko a karkashin jirgin kafin ku harba shi?

2. Wasar Tashi-Karka tashi: Samu rukunin abokai don 'tashi' a zagayen daki, ba tare da taɓa juna ba. Wanda ke labe ya tsaya a wata kusurwa ya kira sunayen abubuwa masu tashi ko marasa tashi. Lokacin da aka kira abun da bai tashi ba (kamar tebur), 'jirage' dole 'su sauka' (zauna). Duk wanda yayi kuskure to ya zama wand zai labe na gaba.

Wannan littafin ya samu ne ta hanyar Pratham Books' dandalin yanar gizo na StoryWeaver. Ana iya saukarwa da fassara abun da ke ciki ta a karkashin lasisi na Creative Commons, kuma ana iya amfani da shi don ƙirƙirar sababbin labarai idanga mai hakin mallaka, kuma a nuna idan an yi canje-canje. Don ƙarin sani game da wannan, da kuma cikakkun sharuɗan amfani da alakantawa, sai a ziyarci wannan hanyar haɗi .

Alakantawar Labari:

Wannan labari: Yaya Jiragen Sama ke Tashi? Rubutawa daga Aditi Sarawagi . Hakkin mallaka © Pratham Books , 2016 An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0.

Sauran Ta'allakawa:

An buga wannan littafin a kan Labarin StoryWeaver na Pratham Books. Bunkasa wannan littafin ya samu tallafin Oracle Giving Initiative. www.prathambooks.org

Alakantawar Zane:

Marfin shafi: Jirgin sama da yarinya , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0.

Shafi na 2: Yarinya tana kallon maiki a sararin samaniya , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 3: Yarinya ta ga malami kamar

agwagwa a cikin tunaninta , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 4: Tsuntsaye a kan waya, Na'urori Masu Tashi , daga Lavanya Karthik hakkin malaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 5: Jirgin sama da yarinya , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 6: Tsuntsaye a sararin samaniya, Yarinya a cikin jirgi , daga Lavanya Karthic hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 7: Injinin Jirgin sama , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 8: Yarinya ta tashi a cikin jirgin sama , daga Lavanya Karthic hakkin malaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 9: Jirgi zai tashi , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 5: Dakin tukin jirgin sama , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 11: Jirgin saman farko na kasar Hindu, lasin matukin jirgi , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Disclaimer: https://www.storyweaver.org.in

/terms_and_conditions

An kiyaye wasu hakkoki. Wannan littafin yana da lasisi mai lamba CC-BY-4.0. Ku na iya kwafa, canzawa, rarraba da yin aikin, har ma don dalilai na kasuwanci, duk ba tare da neman izini ba. Don cikakkun sharuďan amfani da alakantawa, http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ Bunkasa wannan littafin ya samu tallafin Oracle Giving Initiative.

Wannan littafin ya samu ne ta hanyar Pratham Books' dandalin yanar gizo na StoryWeaver. Ana iya saukarwa da fassara da abun da ke ciki ta a karkashin lasisi na Creative Commons, kuma ana iya amfani da shi don ƙirƙirar sababbin labarai idanga mai hakin mallaka, kuma a nuna idan an yi canje-canje. Don ƙarin sani game da wannan, da kuma cikakkun sharuɗan amfani da alakantawa, sai a ziyarci wannan hanyar haɗi .

Alakantawar Zane:

Shafi na 12: Jirgin saman Jet, Sarla Thakral , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Shafi na 13: Yara suna wasa , daga Lavanya Karthik hakkin mallaka © Pratham Books, 2016. An kiyaye wasu hakkoki. Da aka saki a ƙarƙashin lasisin CC BY mai lamba 4.0. Disclaimer: https://www.storyweaver.org.in /terms_and_conditions

An kiyaye wasu hakkoki. Wannan littafin yana da lasisi mai lamba CC-BY-4.0. Ku na iya kwafa, canzawa, rarraba da yin aikin, har ma don dalilai na kasuwanci, duk ba tare da neman izini ba. Don cikakkun sharuɗan amfani da alakantawa, http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ Bunkasa wannan littafin ya samu tallafin Oracle Giving Initiative.

Yaya Jiragen Sama ke tashi? (Turanci)

Sarla ta yi fatan ta na tashi sama kamar maiki ko kamar jirgin sama. Tabbas za ki iya tashi, inji sabuwar malamarta. Anan, Sarla ta sanar da duk abin da ta koya game da tashi da jirgin sama.

Wannan littafin mataki na 3 ne ga yara waɗanda suke shirye don yin karatu da kansu ba tare da taimako ba.

PRATHAM BOOKS

storyweaver

An zamanantar da Littafan Pratham don saƙa sabon babi a cikin tsarin labaran yara a harsuna da yawa. Haɗe yara wuri daya, marubuta, masu zane da masu wallafawa. Yin jingina a cikin malamai, da masu fassara. Don ƙirƙirar zafafan labaran harsuna da yawa masu bayyanannen lasisi don amfanin yaran kasar Hindu da duniya baki daya. Dandali namu na yanar gizo da babu irin shi, StoryWeaver, dandalin wasa ne inda yara, iyaye, malamai da masu kula da ɗakunan karatu zasu iya samun fasaha. Ku zo, ku fara saƙa a yau, kuma ku taimaka mu na wurin samun littafi a cikin hannun kowane yaro!